# Kana cikin Rudani?

Muna bukatan wani malaminSunni ya fayyace mana a karshe su waye Magada Sha biyu, Kalifai, *Amirai* da *Imamai* na gaskiya :

Sanannen malami al-Dhahabi yace a cikin Tadhkirat al-Huffaz, kundi na 4, shafi na 298, da Ibn Hajar al-'Asqalani yace a cikin al-Durar al-Kaminah, kundi na 1, shafi na 67 cewa Sadruddin Ibrahim bin Muhammad bin al-Hamawayh al-Juwayni al-Shafi'i babban malamin Hadith ne. Shi Al-Juwayni ya ruwaito daga Abdullah ibn Abbas (r) daga Annabi (s) wanda ya ce, "**Ni ne shugaban dukkan Annabawa kuma Ali ibn Abi Talib shine shugaban magada na, kuma baya na magada na za su zama sha biyu, na fako daga cikin su Ali ibn Abi Talib ne na karshen su kuma Al Mahdi.**"

Al-Juwayni ya kara ruwatowa daga Ibn 'Abbas (r) daga Annabi (s): "**Tabbas Kalifofi na da magada na da kuma Hujjojin Allah akan halittun shi baya na sha biyu ne. Na farkon su danuwana ne kuma na karshen su da (jika) na ne.**" Sai aka tambaye shi: "Ya Manzon Allah, waye kanin ka?" Ya ce, "**Ali ibn Abi Talib**" Sai kuma suka tambaya, "Kuma waye dan ka?" Sai Annabi (s) ya amsa, "**Al Mahdi**, wanda zai cika duniya da adalci da gaskiya kaman yadda ta cika da zalunci da danniya. Kuma ina rantsuwa da Wanda Ya aiko ni a matsayin mai gargadi da yin albishir, ko da zai rage rana daya a rayuwar duniyan nan, Allah Madaukaki zai ja wannan ranar har sai ya turo dana Mahdi, kuma ya umurci Ruhullah 'Isa ibn Maryam (a) da ya sauko ya yi sallah a bayan sa (Mahdi). Kuma duniya zata cika da hasken annurin sa. Kuma mulkin sa zai mamaye gabashi da yammacin duniya."

Al-Juwayni ya kara ruwaitowa cewa Manzon Allah (s) ya fada: "**Ni da Ali da Hasan da Husaini da tara daga cikin zuriyar Husaini sune tsarkakakku kuma ma'asumai.**"

[Al-Juwayni, Fara'id al-Simtayn, Mu'assassat al-Mahmudi li-Taba'ah, Beirut 1978, p. 160.]

**Cikin dukan mazhabobin Musulunci, Shi'ah Imamiyyah Ithna 'Ashariyyah (Shi'awan Imamai Sha biyu) ne kadai su ka yi imani da wa'yannan mutane Sha biyu sune magada na gaskiya na Annabi (s) kuma sun sami fahimtan Musulunci daga wajen su. In kana so ka karin bayani akan Musulunci na ingantacce, jeka:**

***http://al-islam.org/faq/***

*v1.0*

Jabir ibn Samura ya ruwaito: Na ji Annabi (s) na cewa: "Za a yi There will be **Jagorori Goma**." Sai ya kara da fadin wani jimla da ban ji ba. Mahaifina yace, Annabi ya kara da cewa, "Dukan su daga Kuraishawa ne."
[Sahih al-Bukhari (Bugun Turanci), Hadith: 9.329, Kitabul Ahkam; Sahih al-Bukhari, (Arabic), 4:165, Kitabul Ahkam]

Annabi (s) ya ce:
"Addini (Musulunci) ba zai gushe ba har zuwa Sa'a(Ranan Tashin kiyama), face yana da **Kalifofi Sha biyu**, dukan su daga Kuraishawa."
[Sahih Muslim, (Bugun Turanci), Chapter DCCLIV, v3, p1010, Tradition #4483; Sahih Muslim (Arabic), Kitab al-Imaara, 1980 Saudi Arabian Edition, v3, p1453, Tradition #10]

# Su waye wa'yannanKalifofin Annabi(s) Sha biyu?

| Me Malaman Sunni suka ce: | |
|---|---|
| Ibn al-'Arabi: | Mun kirga Amirai bayan Annabi (s.a.w.s.) azaman sha biyu. Sai muka same su kamar haka: Abu Bakr, 'Umar, 'Uthman, Ali, Hasan, Mu'awiyah, Yazid, Mu'awiyah ibn Yazid, Marwan, 'Abd al-Malik ibn Marwan, Yazid bin 'Abd al-Malik, Marwan bin Muhammad bin Marwan, As-Saffah... Bayan su kuma akwai ashirin da bakwai daga Bani Abbas.<br><br>To, in muka dauki sha biyu kawai daga cikinsu za mu tsaya ne a kan Sulayman. In muka dauki gundarin ma'ana zamu dauki biyar kawai daga cikin su kuma mu kara Kalifofi Shiryayyu guda hudu, da 'Umar bin 'Abd al-'Aziz...<br><br>**Ni ban gane ma'anan wannan Hadisin ba.**<br>[Ibn al-'Arabi, Sharh Sunan Tirmidhi, 9:68-69] |
| Qadi 'Iyad al-Yahsubi: | Yawan Kalifofi sun zarce haka. **Takaita su zuwa sha biyu kuskure ne.** Annabin (s.a.w.s.) bai ce za a yi sha biyu kawai ba ko ba daman kara wasu. Sabo da haka akai yiwuwan a samu kari .<br>[Al-Nawawi, Sharh Sahih Muslim, 12:201-202; Ibn Hajar al-'Asqalani, Fath al-Bari, 16:339] |
| Jalal al-Din al-Suyuti: | **Akwai Kalifofi sha biyu kawai har zuwa Rana Hisabi.** Kuma za su ci gaba da aiki akan gaskiya, ko da ba za su zo a jere ba.<br><br>Mu na iya fahimta cewa hudu daga cikin sha biyun sune Shiryayyun Kalifofi, sai Hasan, sai Mu'awiyah, sai Ibn Zubayr, sai a karshe 'Umar bin 'Abd al-'Aziz. Su takwas kenan. Hudu kenan sukayi saura. Watakil ana iya sa Mahdi, saboda a Abbasiyawa kamar 'Umar bin 'Abd al-'Aziz yake a Umayyawa. Kuma ana iya karawa da Tahir 'Abbasi saboda yayi mulki na adalci. **Har ila yau saura biyu da basu fito ba.** Amma daya daga cikin su shi ne Mahdi, saboda yana daga Ahlul Bayti (a.s.).<br>[Al-Suyuti, Tarikh al-Khulafa, Page 12; Ibn Hajar al-Haytami, Al-Sawa'iq al-Muhriqa Page 19] |
| Ibn Hajar al-'Asqalani: | **Ba wanda yakeda cikakken sani akan (ma'anar) wannan hadisi na Sahih Bukhari.**<br><br>Kuskure ne a ce wa'yannan Imamai za su kasance a waje daya kuma a zamani daya.<br>[Ibn Hajar al-'Asqalani, Fath al-Bari 16:338-341] |

| | |
|---|---|
| Ibn al-Jawzi: | Kalifan farko na Bani Umayya shine Yazid ibn Mu'awiyah kuma na karshe, shine Marwan Al-Himar. **Dukkansu sha uku ne**. **'Uthman, Mu'awiyah and ibn Zubayr basa ciki saboda su Sahabban Annabi (s) ne.** In muka cire Marwan bin al-Hakam saboda cekuce batun kasancewan shi Sahabi ko yana karagan mulki duk da Abdullah ibn Zubayr na da goyon bayan mutane. **Sai mu samu yawan Sha biyu.** … Lokacin da kalifa ya fito daga Bani Umayya, wani babban hargitsi ya taso. Sai da Bani Abbas suka kafa kansu. Saboda haka, yanayin asalin ya canja gaba daya.<br>[Ibn al-Jawzi, *Kashf al-Mushkil*, as quoted in Ibn Hajar al-'Asqalani, *Fath al-Bari* 16:340 from Sibt Ibn al-Jawzi] |
| Al-Nawawi: | Yana kuma iya nufin Imamai sha biyu za su rage a lokacin da Musulunci keda daukaka. Lokacin da Musulunci zai shi ga ko ina.**Wa'yannan Kalifan za su kawo daukakan addini a zamaninsu.**<br>[Al-Nawawi, *Sharh Sahih Muslim* ,12:202-203] |
| Al-Bayhaqi: | **Wannan lamba (sha biyu) ana samun shi har zuwa lokacin Walid ibn 'Abd al-Malik. Bayan wannan, an yi hargitsi da rikici.** Sai daulan Abbasiyawa ya zo. Sai hakan ya kara yawan Imamai. In muka bar wasu ababen da suka auku bayan rikicin, sai yawan su yafi hakan."<br>[Ibn Kathir, *Ta'rikh*, 6:249; Al-Suyuti, *Tarikh al-Khulafa* Page 11] |
| Ibn Kathir: | Duk wanda ya karanta Bayhaqi kuma ya yarda da fadin shi cewa Jama'ah na nufin kalifan da suka zo a yayyanke har zuwa lokacin **Walid ibn Yazid ibn 'Abd al-Malik mai yin ta'adi** ya zo karkashin darasin hadisin da muka ruwaito wanda ya na zargi da kushe irin wa'yannan mutane.<br><br>Kuma in muka yarda da Kalifancin Ibn Zubayr kafun 'Abd al-Malik **yawan zai zama sha shida**. Alhali yawan ya kamata ya zama sha biyu kafun 'Umar ibn 'Abd al-'Aziz. **A irin wannan hanyan Yazid ibn Mu'awiyah za a sa a bar 'Umar ibn 'Abd al-'Aziz.** Amma, an tabbatar da cewa mafi yawan 'ulama sun karbi 'Umar ibn 'Abd al-'Aziz a zaman Kalifa mai gaskiya da adalci**.**<br>[Ibn Kathir, *Ta'rikh*, 6:249-250] |